# God’s Simple Plan of Salvation taken from I Yahaya

## Introduction

I Yahaya 5:13   Na rubuto muku wannan ne, ku da kuka gaskata da sunan Ɗan Allah, domin ku tabbata kuna da rai madawwami.

## 1. Dukan mu mun yi zunubi. Dukan mu mun yi abubuwan da zasu sa ɓacin zuciya ga Allah. Babu wani ɗaya wanda ya zama marar laifi.

I Yahaya 5:16-17   Kowa ya ga ɗan'uwansa yana yin zunubin da bai kai ga mutuwa ba, sai ya yi masa addu'a. Saboda mai addu'ar nan kuwa, Allah zai ba da rai ga waɗanda suka yi zunubin da bai kai ga mutuwa ba. Akwai zunubin da yake na mutuwa. Ban ce a yi addu'a domin wannan ba.  Duk rashin adalci zunubi ne. Akwai kuma zunubin da ba na mutuwa ba.

1 Yahaya 3:6   Kowa da yake a zaune a cikinsa, ba ya aikata zunubi. Kowa da yake aikata zunubi, bai taɓa ganinsa ba, bai ma san shi ba.




**We are all sinners!**

## 2.   Tana koyar mana game da abubuwan da zunubi yakan haifar –

I Yahaya 5:19   Mun sani mu na Allah ne, duniya duka kuwa tana hannun Mugun.

I Yahaya 5:12   Duk wanda yake da Ɗan, yana da rai. Wanda ba shi da Ɗan Allah kuwa, ba shi da rai.

1 Yahaya 3:15   Kowa da yake ƙin dan'uwansa, mai kisankai ne. Ƙun kuwa sani ba mai kisankan da yake da rai madawwami a zauna tare da shi.

# 3. Yesu Kiristi ya mutu dominmu! Mutuwar Yesu ta biya don farashin zunubanmu. Tashin Yesu daga matattu ta gwada cewa Allah ya amshi mutuwar Yesu a matsayin biyarwa don zunubanmu.

1 Yahaya 4:10 Ta haka ƙauna take, wato, ba mu ne muka ƙaunaci Allah ba, sai dai shi ne ya ƙaunace mu, ya aiko Ɗansa, hadayar sulhu saboda a gafarta zunubanmu.



## Christ died for sinners!

1 Yahaya 4:2-3 Ta haka za ku san Ruhun Allah, wato, duk ruhun da ya bayyana yarda, cewa Yesu Almasihu ya bayyana ne da jiki, shi ne na Allah. Duk ruhun kuwa da bai bayyana yarda ga Yesu ba, ba na Allah ba ne, wannan shi ne ruhun magabcin nan na Almasihu wanda kuka ji zai zo, a yanzu ma har yana duniya.

I Yahaya 5:11 Wannan kuma ita ce shaidar, cewa Allah yā ba mu rai madawwami, wannan rai kuwa yana cikin Ɗansa.

# 4. Ba zamu iya ceton kanmu ba.

Actes 4:12 Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk duniyar nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto."

Éphésiens 2: 8-9 Domin ta wurin alheri ne aka cece ku saboda bangaskiya, wannan kuwa ba ƙoƙarin kanku ba ne, baiwa ce ta Allah, ba kuwa saboda da aikin lada ba, kada wani ya yi fariya.

Tite 3:5 sai ya cece mu, ba don wani aikin adalci da mu muka yi ba, a'a, sai dai domin jinƙan nan nasa, albarkacin wankan nan na sāke haihuwa, da kuma sabuntawar nan ta Ruhu Mai Tsarki,

# 5. Saboda mutuwar Yesu a madadinmu, duk abin da ya kamata muyi shine bangaskiya cikinsa, muna amincewa da mutuwarsa a matsayin biya don zunubanmu – kuma zamu sami ceto!

Romawa 10:9-10,13 Wato, in kai da bakinka ka bayyana yarda, cewa Yesu Ubangiji ne, ka kuma gaskata a zuciyarka Allah ya tashe shi daga matattu, za ka sami ceto. Domin da zuci mutum yake gaskatawa yă sami adalcin Allah, da baki yake shaidawa ya sami ceto. "Duk wanda kuwa ya yi addu'a da sunan Ubangiji zai sami ceto."

I Yahaya 5:14-15 Wannan ita ce amincewarmu a gabansa, wato, in mun roƙi kome bisa ga nufinsa, sai ya saurare mu. In kuwa muka san kome muka roƙa yana sauraronmu, mun tabbata mun sami abin da muka roƙa a gare shi ke nan.



*Idan kana son ka karɓi Yesu Kiristi a matsayin mai cetonka, ga samfurin addu'a anan. Ka tuna, faɗar wace nan addu'a ko wata addu'a dabam ba zai cece ka ba. Amincewa ce kaɗai cikin Kiristi wanda zai iya cece ka daga zunubi. Wace nan addu'a, hanya ce mai sauƙi a furta ga Allah bangaskiyarka a cikin Sa kuma ka gode masa don ya tanadar maka da ceto.*



**”Allah,**

**na sani cewa nayi zunubi gareka kuma na cancanci hukunci. Amma Yesu Kiristi ya ɗauki hukuncin da ya cancance ni, don ta wurin bangaskiya a cikinsa in sami gafartawa. Na juyo daga zunubaina kuma na sa amincewa tawa a cikinka don ceto. Na gode maka don alherinka mai ban mamaki da kuma gafara – kyautar rai madawwami! Amin!”**

**Amazing Grace Publishing * PO Box 1963 * Joshua TX 76058 * 817-426-1828 * E-Mail JamesAV@aol.com**